Ku yaƙi mushrikai da dukiyoyinku da rayukanku da kuma harsunanku

Daga Anas - Allah Ya yarda da shi - cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ku yaƙi mushrikai da dukiyoyinku da rayukanku da kuma harsunanku".
[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Nasa'i haka Ahmad suka ruwaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi umarni da yaƙar kafirai, da yin ƙoƙari a fuskantarsu ta kowace hanya gwargwadan iko dan kalmar Allah ta zama ita ce maɗaukakiya, daga hakan: Na farko: Ciyar da dukiya a yaƙarsu; na siyan makamai da ciyarwa ga mayaƙa da makamancin hakan. Na biyu: Fita da rai da jiki dan haɗuwa da su da kuma tunkuɗesu. Na uku: Da kiransu ga wannan Addinin da harshe, da tsaida hujja akansu, da tsawatar da su da yi musu raddi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/64597